KOMAI NISAN JIFA III

**EPISODE 4**

<u>Characters</u>

*Laraba*

*Nurse Maria*

*Asabe*

*Inna*

*Tina*

*Hannah*

**EPISODE 4, SCENE 1**

*Northern Kaduna. Mid-Morning. Health Centre.*

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |
| 2. | **SFX:** | **<u>SOUND OF KNOCKING ON DOOR FOLLOWED BY SOUND OF ALREADY AJAR DOOR OPENING</u>** |
| 3. | **NURSE MARIA:** | **(COMING ON-MIC, UPBEAT)** Kwon Kwon! Nice nars Maria, ke ce nars Laraba ko. |
| 4. | **LARABA:** | E, nice, na fito da sauri domin in tabbatar da kayakin tazaharar haihuwan, kafin mu soma ganin masu jiyyan. |
| 5. | **MARIA:** | **(LAUGHS)** Wai Laraba, kina daukar wannan sabon aikin naki sosai fa, kada ki damu kan ki kin san ke sabuwar zuwa ce fa…. |

6. **LARABA:** Saboda haka nake son in yi aiki da kyau ai Nars Maria.

7. **MARIA:** **(LAUGHING)** Ba sai ki kira ni nars ba, anan ba mu yi haka, ke dai ki kira ne maria kawai, damar muna ta jiran isowar ki.

8. **LARABA:** **(NERVOUS)** Haba? Me yasa?

9. **MARIA:** Kin san rayuwa ai, ki sabuwar zuwa ce, muna son mu gan ki ai.

10. **LARABA:** **(UNCOMFORTABLE)** Hmmm, toh, ni ba ni da wani abin a zo a gani ai.

11. **MARIA:** **(LAUGHS MOCKING)** Ke dai ki kyale ne in yanke hukuncin, mun dai san kin dade a wanan aikin.

12. **LARABA:** Gaskiya ne Maria, wannan ba shine wurin aiki na na farko ba.

13. **MARIA:** **(AMUSED)** Na ga alama, toh, ina kike aiki kafin ki taho nan?

14. **LARABA:** **(MUMBLING)** Bana tsamanin za ki san asibitin, asibitin na Zaria

15. **MARIA:** Lalai, toh me ya sa kika zo nan, mai gidan ki yak aura ne?

16. **LARABA:** **(UNCOMFORTABLE)** A gaskiya bani da aure Nars Maria.

17. **MARIA:** **(SURPRISED)** Haba? Ba ki da aure? Me yasa?

18. **LARABA:** **(BECOMING UPSET)** Ban dai yi aure tukunna ba, ba wata dalili.

19. **MARIA:** **(AMUSED)** Ina ganin ba ki son dai ki fada min. amma kada ki damu, zan same labarin daga gare ki in an jima.

20. **LARABA:** Ba wani labara ai Nars Maria.

21. **MARIA:** **(LAUGHING)** Toh, Laraba, amma dai nasan masu zurfin ciki su ke da abin da suke boyewa.

22. **LARABA:** **(TRYING TO CHANGE THE SUBJECT)** Gaskiyar ki Nars Maria, ni dai abin da nake son sani shine yaya aikin yake anan?

23. **MARIA:** Aikin ba laifi, muna da likita mai zuwa sau biyu a sati, ranakun talata da alhamis domin ganin masu jinyya, wato Dacta Daoud.

24. **SFX:** **<u>SOUND OF METALIC JARS/POTS BEING OPENED AND CLOSED</u>**

25. **LARABA:** **(DISTRACTED)** Haba? Aiki da shi da dadi?

26. **MARIA:** **(EXCITED)** Dacta Daoud yana da kirki, yana kuma da farin jinni, dogo, kyakyauwa kuma bashi da aure.

27. **SFX:** **<u>SOUND OF PAPERS RUSTLING AS LARABA LOOKS THROUGH FILES</u>**

28. **LARABA:** **(MORE DISTRACTED)** Yayi kyau ai….

29. **MARIA:** **(STILL EXCITED)** Sosai kam. Baki ma sani ba Laraba, duk yan matan suna son shi, amma baya da sha'awar ko guda daga ciki su.

30. **LARABA:** **(POLITELY CUTS IN)** Maria nagode da bayannin, amma ina ganin ya kamata in chi gaba da kula da masu jiyya yanzu.

**EPISODE 4, SCENE 2**

*Northern Kaduna. Mid-Morning. Health Center.*

31. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**
32. **SFX:** **<u>KNOCK ON DOOR</u>**
33. **LARABA:** **(CALLING OUT)** Shigo ciki
34. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING</u>**
35. **LARABA:** Sanu da zuwa, Ina yini, sunnana Nars Laraba, kice malama Asabe.
36. **ASABE:** **(IMPRESSED)** Wai, Nars, har kin san suna na? duk da cewa yanzu muke haduwa?
37. **LARABA:** **(SMILES)** E, Malama Asabe, nayi nazarin katin ki domin in fahimci tarihin zuwan ki, saboda kada mu bata lokaci.
38. **ASABE:** Nars Laraba, ke dai sabuwar zuwa ce ban taba ganin ki anan asibitin ba.
39. **LARABA:** Hakika, Malama Asabe, Ban jima da zuwa ba
40. **ASABE:** kina iya kira na Asabe don Allah Nars Laraba, ina jin kamar wata tsohuwa in ki k ace min malama.
41. **LARABA:** **(LAUGHING)** Toh Asabe, na ga cewa kin saya IUD kusan shekara daya kenan, yau me za'a yi miki.
42. **ASABE:** **(NERVOUSLY)** Na'am Nars Laraba, ina tsamanin akwai matsala fa yanzu.
43. **LARABA:** **(SURPRISED)** Matsalla? Don allah ki kara min bayani.

44. **ASABE:** **(WORRIED)** Toh nars, an fada min cewa in dinga duba zaren IUD lokuta-lokuta, da na duba na karshen ban gan zaren ba.

45. **LARABA:** Babu matsala Asabe, ba zai yu IUD y abaci gaba daya ba, kilar IUD ya shige ciki sosai ko kuma zaren yayi laushi.

46. **ASABE:** **(AGITATED)** Wai! Babbar Magana kenan ai nars.

47. **LARABA:** **(SOOTHING)** Asabe, samsam. Bara in duba mi ki daga nan sai mu san abin da za muyi.

48. **ASABE:** Ah nars, ina fatan babu matsalla fa, ina jin dadin amfani da wannan hayan tazarar haihuwar fa, b azan so in daina amfani da shi ba.

49. **LARABA:** Asabe, kada ki damu! Na tabbata bazai kai haka ba, irin haka na faruwa. Ba zai kai har sai kin daina amfani dashi ba.

50. **ASABE:** Hmmm Laraba, ba ki san yadda amfani da wannan hanyoyin tazarar haihuwa na zamani ya chanja min rayuwa ta ba.

51. **LARABA:** Haba?

52. **ASABE:** **(EXCITED)** Ah gaskiya. Nars, da chan kowace shekara ina haihuwa ba hutu, ba san cewa akwai hanyoyin bada tazara masu inganci ba.

53. **LARABA:** Hanyoyin tazarar haihuwa na zamani suna bada damar wa mata su sami damar hutu tsakanin haihuwa da daukar wani ciki, wanda

hakan zai sa su zama cikin koshen lafiya ma iyalen su da su kansu.

54. **ASABE:** Gaskiya ne, Maigida na ma ya same sauki, ya rasa aikin shi kusan shekara daya kenan kinsan ba zai dace in same juna biyu ba kuma.

55. **LARABA:** Hakika, hanyoyin tazarar haihuwa na zamani suna taimaka wa maza wajen kula da iyalin sa ida ya kamata.

56. **ASABE:** **(SADLY)** Duk da cewa abubuwa basu da sauki a gare mu, tababatar da cewa ban samu juna biyu da ba mu shirya ma ba, ai muna taimaka wa wurin rage nauyi ma masu tallafa mana.

57. **LARABA:** **(COMFORTING)** Na tabbata, ai basu damuwa da hakan. **(CHANGING THE SUBJECT)** Toh, ya yaran ki? Su hudu ne ko?

58. **ASABE:** Suna lafiya. **(SURPRISED)** Amma yak i ka sani ne, Nars Laraba? **(PAUSES)** Oh, kin karata kati na.

59. **LARABA:** **(LAUGHING)** E, kada mu in dau lokacin ki dayawa, nasan an kusan tashi daga makaranta.

60. **ASABE:** **(LAUGHING)** Gaskiyan ki, na fiye surutu ko, maigida na yana fada min, dole ne in hanzarta in tafi gida.

61. **LARABA:** **(LAUGHS)** Amma ba laifi ai, jama'a na cewa ina da shiru shiru sosai kuma ba kyau.

62. **SFX:** **<u>SOUND OF CHAIRS SCRAPING THE GROUND AS THE TWO WOMEN RISE</u>**

63. **LARABA:** Toh Malama Asabe,don Allah ki kwanta in duba miki zaren IUD.

64. **ASABE:** Hmm, Nars Laraba, da suka gaya min cewa wai zan ga sabuwar nars yau, na damu amma yanzu ina murna muna da nars mai fara da kirki kamar ke a al'umar mu

65. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 4, SCENE 3**

*Afternoon. Hannah and Danjuma's Residence.*

66. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING</u>**

67. **SFX:** **<u>AND HIGH HEELED SLIPPERED FOOTSEPS COMING ON MIC</u>**

68. **HANNAH:** **(ON-MIC)** Toh Tina, gad akin, ina fatan za ki so dakin

69. **TINA:** **(CALLING)** Kai, yayi kyau kwarai, ban san zan sami daki mai kyau haka ba ai.

70. **HANNAH:** Karamin daki ne ai, ki yi hakuri da shi.

71. **TINA:** **(CUTS IN)** Wai! Hannah, ai ya fi daki na agidan kawu, kuma muna tare da wasu ma

72. **HANNAH:** Toh Tina, an kuma kamala duk shirye shirye a kamfanin Danjuma.

73. **TINA:** Haba?

74. **HANNAH:** E, mu tautauna da Danjuma, yace za ki yi soma "ITin" sati mai zuwa, kuma za ki zauna tare da mu har sai kin kamala ITin.

75. **TINA:** **(EXCITED)** Ah Hannah, nag ode sosai. Damar ina ta tunanin yadda zan sami muhalli a cikin gari .

76. **HANNAH:** Haba, ke ai, yar uwa ce, muna so kin sami kwanciyar hankali anan.

77. **TINA:** Na gode kwarai **(WORRIED)** Ban sani ba ko

78. **HANNAH:** na'am? Tina ga wurin zama. Menene? Akwai wani abun da keki bukata ne?

79. **SFX:** **<u>SOUND OF BED CREAKING AS THE TWO GIRLS SIT</u>**

80. **TINA:** Daman. Ina cewa ko zan iya dinga bin yaya Danjuma zuwa wurin aiki, ko zan dan adana wani abu daga cikin kudin mota ta.

81. **HANNAH:** **(LAUGHS)** Shike nan, Tina? Dubi yadda ki ka ji tsoron tambayya, kada ki damu zan tautauna da danjuma sai in gaya miki, ko?

82. **TINA:** Toh. Okay. **(PAUSES)** Hannah, amma dan lokacin nan da nake nan kamar ke da Maigidan ki kun shaku sosai, kamar komai sai kun tautauna tare.

83. **HANNAH:** **(HAPPY)** Eh Tina. Mun aminci mu dinga yanke hukunci tare, muna ganin hakan zai sa mu sake shakuwa sosai.

84. **TINA:** Hmmm, ni dai abinda na ke gani, zaman ku tamakar wanda muke kallo a finafini.

85. **HANNAH:** **(AMUSED)**Hmmm Tina, ni ban san zanchin da kike yi ba, bari in je in soma girki, maigida ya kusan ya dawo.

86. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**EPISODE 4, SCENE 4**

*Early Afternoon. Hajiya Inna's Residence.*

87. **SFX:** **SOUND OF CHILDREN PLAYING**

88. **ASABE:** **(COMING ON MIC)** Ah, hajiya sannu, Barkan dai.

89. **INNA:** **(ON MIC)** Asabe, har kin dawo daga asibitin? Ban yi zaton za ki dawo da wuri ba fa, komai da lafiya ko?

90. **ASABE:** Hajiya Inna, sannu da kokarin da kika yi wajen duba yaran, komai lafiya, na dawo da wuri saboda sabuwar nars din da aka kawo, nars Laraba.

91. **INNA:** **(CONFUSED)** Sabuwar nars? Toh?

92. **ASABE:** **(EXCITED)** Hajiya Inna, ai sai kin hadu da ita ma, tana da kirki, ta iya kula da mutun kuma a naste take…

93. **INNA:** **(AMAZED)** Asabe, kamar ba ke ba, yadda kike Magana a kan bakuwa.

94. **ASABE:** Hajiya, akwai wanni abu game da ita! Tana da kirki da kula kamar ba bakuwa ba

95. **INNA:** Haba?

96. **ASABE:** Toh, ki ji, saboda ta san ina da yara a makaranta, tayi kokarin kamala da ni domin in dawo da wuri in same yarana.

97. **INNA:** Abin da ki ke fada min ta zo daidai da abin da MaiUngwa ya fada min, tana da tunani.

98. **ASABE:** **(PROUDLY)** Ah Inna, tun da mai ungwa ma yana yabba  mata, kin san ai Nars Laraba ai alherini ga al'umar mu.

99. **INNA:** Hmm Asabe, yadda kike Magana akan wannan sabuwar nars din haka, ina son in gamu da ita.

100. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**